Kada harshenka ya gushe yana ɗanye daga ambatan Allah

Daga Abdullahi ɗan Busr - Allah Ya yarda da shi - cewa wani mutum ya ce: Ya Manzon Allah lallai shari'un musulunci haƙiƙa sun yi mini yawa, ka sanar dani wani abu wanda zan rataya da shi, sai ya ce: "Kada harshenka ya gushe yana ɗanye daga ambatan Allah".

[Ingantacce ne] [Tirmizi da Ibnu Majah da Ahmad Suka ruwaito shi]

Wani mutum ya kai ƙara wurin Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - cewa nafilifilin ibadu sun yi masa yawa har ya gajiya daga yin su saboda rauninsa, sannan ya tambayi Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya shiryar da shi ga wani aiki mai sauki mai jawo lada mai yawa wanda zai rataya da shi ya yi riƙo da shi. Sai tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya nunar masa harshensa ya zama ɗanye mai motsawa saboda dawwamar ambatan Allah - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka - a kowane lokaci da hali; na tasbihi da tahmidi da istigafari da addu'a da makamancin hakan.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/4716